
# Fiqihun ibada a cikin hotuna

Karantar da hukunce-hukuncen musulunci a sauqaqe

Tsarki | Sallah | Azumi | Zakkah | Hajji



**Dr.Abdullah Bahammam**

tarjama

Muhammad Rabi'u Umar Musa R/lemo

bita

Dr. Muhammad Sani Umar Musa
Shaikh Nura Sani Muhammad

## Tsarki Da Ruwa

https://www.al-feqh.com/ha



# Tsarki Da Ruwa



**Tsarki**

- Tsarki
- Ma'anar Tsarki
- Kashe-Kashen Tsarki
- 1 – Tsarki na ɓoye
- 2 – Tsarki na Zahiri
- Ruwa
- Rabe – Raben Ruwa
- 1- Ruwa mai tsarki mai tsarkakewa
- 2- Ruwa mai najasa

## Tsarki


**Ma'anar Tsarki A Larabci.**

Tsafta Da Tsarkaka Daga Kazanta

**Ma'anar Tsarki A shari'a**

Kawar da kari da gusar da Najasa

## Kashe – Kashen Tsarki






https://www.al-feqh.com/ha

## Kashe – Kashen Tsarki

### 1. Tsarki Na Ɓoye

Shi ne tsarkake zuciya daga shirka da sabo, da duk wani abin da yake bata zuciya, babu yadda tsarki zai tabbata matukar akwai shirka a cikin zuciya, kamar yadda Allah ya ce,{Yaku wadanda suka yi imani ku sani cewa Mushirikai najasa ne, kada su kusanci masallaci mai alfarma daga wannan shekarar, idan kuna jin tsoron talauci to da sannu Allah zai azurta ku daga falalarsa in ya so. Haƙiƙa Allah Masani ne Mai hikima}[At-Tauba : 28].

Manzon Allah (ﷺ) ya ce,«Mumini ba ya zama najasa».

### 2-Tsarki Na Zahiri

Shi ne tsarkake jiki daga abubuwan da suke warware alwala da najasa, ya kasu gida biyu :

https://www.al-feqh.com/ha



## 1-Tsarkin Kari

Kari shi ne : Abin da yake hana mutum yin ibadar da aka sharɗanta tsarki a cikinta, kamar sallah, dawafi da waninsu. Kari ya kasu kashi biyu :



Kari yana hana yin sallah.

## Karamin Kari

Shi ne wanda yake wajabta yin alwala, kamar fitsari da kashi da sauran abubuwan da suke warware alwala. Tsarki daga kari yana samuwa ne ta hanyar alwala.

Allah ya ce, {Yaku waɗanda kuka yi imani idan kun tashi za ku yi sallah, to ku wanke fuskokinku da hannayenku zuwa gwiwar hannu, ku shafi kawunanku ku wanke kafafunku zuwa idon sawu} [Al-ma'ida :6].



Alwala tsarki ce daga ƙaramin kari

## Babban Kari

Shi ne wanda yake wajabta wanka, kamar janaba, haila, da wanin haka, ana tsarkaka daga gare shi ta hanyar wanka.

Allah ya ce, {Idan kuna da janaba to ku yi tsarki} [Al-ma'ida : 6].

## 2-Tsarkaka Daga Najasa

Gusar da najasa wajibi ne, saboda faɗin Allah Maɗaukakin Sarki {Ka tsarkake tufafinka} [Al-Muddassir 4]. Da faɗin Manzon Allah (ﷺ) «Mafi yawancin azabar ƙabari daga rashin yin tsarki ne idan an yi fitsari» Da faɗinsa (ﷺ) «Idan ɗayanku ya zo masallaci to ya duba takalmansa, idan ya ga ƙazanta ko najasa to ya goge, sannan ya yi sallah da su».



Tsarkin wurin sallah



Tsrkin jiki



Tsarkin Tufa

# Kashen Ruwa

## Ruwa
### Kashe-Kashen Ruwa

- Ruwa mai tsarki
  - Tsantsar Ruwa
  - Ruwan da aka yi amfani da shi
  - Ya gauraya da najasa amma ba ta canza shi ba Ibn Majah ne ya rawaito shi Abu Dawud ne ya rawaito shi
  - Ya gauraya da abu mai tsarki
- Ruwa mai najasa (wato ruwan da ya hađu da najasar da ta canza shi).

## Kashe-Kashen Ruwa

### Na farko : Ruwa Mai tsarkake wa

Shi ne ruwan da najasa ba ta canza kamaninsa, ko danđanonsa ko ƙanshinsa ba, kamar:

### 1-Ruwa Tsntsa

Shi ne ruwan da yake akan siffar shi da aka halicce shi da ita, kamar ruwan sama, ko ƙanƙara, ko raɓa, ko kuma wanda yake gudu ne a bayan ƙasa, kamar ruwan teku, da ƙoramu da na sama, da rijiya. Allah Mađaukakin Sarki ya ce,{Mun saukar da ruwa mai tsarki daga sama}[AlFurƙan : 4]

Allah Mađaukakin Sarki ya ce,{Yana saukar muku da ruwa daga sama don ya tsarkake ku da shi} [Al-anfal : 11] Hakanan Manzon Allah (ﷺ) yana addu'a yana cewa:«Ya Allah ka wanke ni daga zunubaina da raɓa da ruwa da ƙanƙara» (Bukhari da Muslim ne suka rawaito shi).

Manzon Allah ya ce dangane da ruwan teku «Shi ruwa ne mai tsarki, kuma mushensa halal ne» (Ahmad da Abu Dawud ne suka rawaito shi).


Ruwan sama


Koramu


Rijiyoyi


Tekuna



https://www.al-feqh.com/ha

https://www.al-feqh.com/ha



https://www.al-feqh.com/ha

## 2 - Ruwan Da Aka Yi Amfani Da Shi

Shi ne ruwan da yake zubo wa daga jikin gaɓɓan mai al'awa ko mai wanka, babu laifi a yi amfani da shi wajen yin tsarki, saboda abin da ya tabbata daga Abdullahi ɗan Abbas Allah ya yarda shi ya ce, «Ɗaya daga cikin matan Annabi (ﷺ) ta yi wanka wata kwatanniya, sai Manzon Allah (ﷺ) ya zo yana son ya yi alwala da sauran wannan ruwan, sai ta ce masa, Ya Manzon Allah ni fa ina da janaba sai ya ce, Ai lalle wannan ruwan bai zama najasa ba» (Tirmizi ne ya rawaito shi).

## 3-Ruwan Da Ya Gauraya Da Abu Mai Tsarki

Shi ne ruwan da ya gauraya da wani abu mai tsarki, kamar ganyen bishiya, ko turɓaya, ko ya haɗu da tsatsa, kamar ruwan tankuna, amma abin da ya haɗu da shi bai yi tasiri a kansa ba, tasirin da zai fitar da shi daga sunanshi na ruwa.

Saboda abin da Manzon Allah (ﷺ) ya faɗa wa matan da suke shirya 'yarsa wadda ta mutu, ya ce musu :«Ku wanketa da ruwa da magarya sau uku, ko biyar, ko fiye da haka in akwai buƙata Magarya: A nan ana nufin ganyen bishiyar magarya. ana dandaƙa shi a yi amfani da shi wajen tsaftace abubuwaKu sanya Kafur a wanki na ƙarshe» (Bukhari da Muslim ne suka rawaito shi).



Tsatsar tankunan ruwa



Ruwan da ya gauraya da ganyen bishiya



Ruwa da ya haɗu da ƙasa

## Canzawar Ruwa

Idan ruwa ya canza da abin da ya yi masa tasiri, ya fitar da shi daga kasancewarsa ruwa zuwa wani abu daban, kamar ruwan shayi, lemo, ko waninsu, to ba ya halatta a yi tsarki da shi, saboda ba a kiransa ruwa.

https://www.al-feqh.com/ha





Romo



Shayi



Tauwada



Lemo

### 4-Ruwan Da Ya Gauraya Da Najasa Amma Ba Ta Canza Shi Ba

Shi ne ruwan da najasa ta faɗa masa, kamar fitsari, ko mushe da makamantansu, amma najasar ba ta canza wani abu daga siffofin ruwan ba, to wannan ruwan mai tsarki ne, saboda faɗar Manzon Allah (ﷺ) game da wata rijiya mai suna "Buda'a" ya ce, «Lallai ruwanta mai tsarki ne, babu abin da ya mayar da shi najasa» (Ahmad da Tirmizi ne suka rawaito shi). Abin nufi, mutane sun kasance suna jefar da ƙazanta kusa da wannan rijiyar, sai ruwan sama ya kora ta cikin rijiyar, amma ruwan saboda yawansa waɗannan abubuwa ba sa tasiri a cikinsa, ba ya canza wa.

## Na Biyu : Ruwa Mai Najasa

Shi ne wanda wani abu na najasa ya faɗa cikinsa, kamar fitsari, ko mushe, ya kuma canza ɗaya da cikin siffofinsa uku – ƙanshinsa, ko ɗanɗanonsa ko launinsa – to wannan ruwan ya zama najasa da ijma'in malamai, ba ya halatta a yi amfani da shi.



https://www.al-feqh.com/ha

https://www.al-feqh.com/ha





Mushe wanda ya canza ruwa



Mushe ya faɗa ruwa bai canza shi ba

## Mas'aloli

1. Asali shi ne kowanne ruwa mai tsarki ne, saboda haka idan aka samu ruwan da ba a sani ba mai tsarki ne ko mai najasa ne? to asali shi ne mai tsarki ne, bai kamata a ɗorawa kai wata wahala ba.

2. Ya halatta a yi alwala da ruwan zamzam, saboda Manzon Allah ya sa an kawo masa ruwan zamzam cikin guga ɗaya, ya sha ya yi alwala da shi"



https://www.al-feqh.com/ha